# HUƊUBAR JUMA'A

2023/6/23 م

١٤٤٤/١٢/٥هـ






GABATARWAR BABBAN MALAMI DAKTA

**ABDULMUHSIN ƊAN MUHAMMAD ALƘASIM**

LIMAMI KUMA MAI HUƊUBA
A MASALLACIN ANNABI MAI DARAJA


TAKEN HUƊUBAR

# AYUKKAN KWANA GOMA NA ZUL-HIJJAH

# AYUKKAN KWANAKI GOMAN ZULHIJJA[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman gafararSa, kuma muna neman tsarinSa daga sharrukan kawunanmu da kuma zunubban ayukkanmu, duk wanda Allah Ya shiryar to babu mai ɓatar da shi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya face Allah Shi kaɗai baShi da abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da sahabbansa kuma da Aminci mai yawa.

**Bayan haka:**

Kuji tsoron Allah -ya ku bayin Allah- haƙiƙanin jin tsoro, kuma ku kiyaye Shi a cikin sirri da kuma ganawa.

**Yaku Musulmi:**

Lokuta na alkhairi suna maimaituwa ga bayi na daga falalar Allah da karamcinSa; da zarar wani

[1] Anyi wannan huɗubar ranar Juma'a, biyar ga watan Zul-hijjah, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba'in da huɗu bayan hijirah, a masallacin Annabi.

aikin bauta ya ƙare sai wata bautar daban ta biye mata; domin su wanke dauɗarsu a cikinta, kuma darajojinsu su ɗaukaka a cikinta.

Kuma haƙiƙa wasu kwanaki goma masu albarka sun lulluɓemu, sune mafiya alkhairin kwanaki kuma mafiya falalarsu, kuma mafiya ɗaukakarsu da girmansu, Allah Yayi rantsuwa da su, sai Yace:

﴿وَالفَجْرِ * وَلَيَالٍ عَشْرٍ﴾

"Ina rantsuwa da lokacin alfijir*da darare goma", Mas'ruuƙ Allah Ya jiƙansa ya ce: "sune kwanaki goman layya, mafiya falalar kwanakin shekara", kuma suna daga cikin kwanakin Allah haramtattu, kuma cikamakon watanni sanannu, waɗanda Allah Yake cewa game dasu:

﴿الحَجُّ أَشْهُرٌ مَّعْلُومَاتٌ﴾

"Hajji watanni ne sanannu" Ka'ab Allah Ya jiƙansa ya ce: "mafi soyuwan watanni a wurin Allah itace zulhijjah, kuma mafi soyuwa a wurin Allah a cikin zulhijjah sune goman farko", wuninta sun su falala sama da wunin goman ƙarshe na Ramadana; Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "mafiya falalar kwanakin duniya: sune kwanaki goma"[Ibn Hibban ya ruwaito shi], Shehun

Musulunci Allah Ya jiƙansa ya ce: "wuninnika goma na Zul-hijjah sun fi falala sama da wuninnika goma na Ramadana, kuma dararen goman ƙarshe na Ramadana sun fi falala sama da dararen goma na Zul-hijjah".

Kuma falalar goma na Zul-hijjah: domin tattaruwan manyan ibadoji ne a cikinsu -irin sallah, azumi, sadaka, hajji-, kuma haka basa samuwa a cikin waninsu.

Kuma banbantan falala tsakanin darare da wuni yana janyo hankali kan ribatar alkhairin dake cikinsu, kuma yana daga cikin ribatar kwanaki goman: yawaita ayukka na ƙwarai a cikinsu; domin ayukka na ƙwarai a cikinsu sunfi soyuwa ga Allah sama da irin aikin idan ya kasance a cikin wasunsu; Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "babu wani aiki a cikin wasu kwanaki da ya kai falalar aiki a cikin waɗannan" suka ce: koda jihadi ne? Yace: koda jihadi ne; sai dai mutumin da ya fita da ransa da dikiyarsa, amma bai dawo da wani daga cikinsu ba"[Bukhari ya ruwaito shi], Ibn Rajab Allah Ya jiƙansa ya ce: "kuma haƙiƙa wannan hadisin yayi nunin cewa aiki a cikin kwanaki goman sun fi soyuwa a wurin Allah sama da aiki a cikin dukkan kwanakin duniya ba tare togace wani abu daga cikinsu ba" Kuma haƙiƙa Magabata Allah

Ya jiƙansu sun kasance suna dagewa wajen ayukka na ƙwarai a jikinsu, "Saeed bn Jubair Allah Ya jiƙansa ya kasance idan goman Zulhijja suka shigo ya na dagewa dagewar da ya kai baza'a iya yin irinsa ba".

Kuma daga cikin falalar Allah da karamcinSa: kasantuwar ayukka na bauta a cikin waɗannan kwanaki goma nau'i-nau'i ne, kuma yana daga cikin abinda aka shar'anta a cikinsu yawaita ambaton Allah; Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce:

﴿وَيَذْكُرُوا اسْمَ اللَّهِ فِي أَيَّامٍ مَعْلُومَاتٍ﴾

"Kuma su ambaci sunan Allah a cikin kwanaki sanannu" Ibn Abbas Allah Ya yarda da su ya ce: "sune kwanaki goma", kuma ambatonSa Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi a cikinsu yana daga cikin mafificin neman kusanci; Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "babu wasu kwanaki mafiya girma a wurin Allah ko mafi soyuwa a gare Shi yin aiki a cikinsu sama da waɗannan goman; to ku yawaita yin hailala a cikinsu da takbiri da tahmidi"[Ahmad ya ruwaito shi], Annawawiy Allah Ya jiƙansa ya ce: "Anso yawaita yin zikirori a cikin waɗannan goman sama da wasunsu na kwanaki, kuma anso a cikin haka yawaitawa sama da sauran kwanakin a ranar

Arafah", kuma mafi falalar zikiri shine karatun lattafin Allah; domin shine shiriya kuma haske bayyananne.

Kuma shi kabbara na koda yaushe a kowane lokaci yana daga cikin tambarori na kwana goman Zul-hijjah, kuma, "Ibn Umar da Abu Hurairah Allah Ya yarda da su sun kasance suna fita zuwa kasuwa a kwanaki goman, suna yin kabbara mutane suna yin kabbarar da kabbararsu"[Bukhari ya ruwaito shi a ta'liƙance].

kuma an shar'anta yin kabbara iyakantacciya a bayan salloli farillai, tun daga ketowar alfijirin ranar Arafah ga alhazai da waɗanda basu ba har zuwa la'asar ɗin ranar ƙarshe ta busar da nama.

Kuma sadaka aiki ne na ƙwarai, da ita ake yaye baƙin ciki, kuma damuwoyi suke gushewa, kuma mafi alkhairin abinda ya kasance lokacin buƙata tare da darajar lokaci, Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "mai tsayuwa da al'amuran bazawara da matalauci; kamar mai jihadi ne a tafarkin Allah" kuma ina zoton ya ce- kamar mai tsayuwar dare ne wanda baya yankewa, kuma kamar mai azumi ne wanda baya shan azumi"[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma yana daga cikin abinda ake so a cikin kwanaki goman: azumtar kwanaki taran farko daga cikin watan, Annawawy Allah Ya jiƙansa ya ce: "Mustahabbine mustahabbanci mai tsanani", kuma azumtar ranar Arafah "yana kankare zunubin shekarar da ta gabata da shekara ta gaba"[Muslim ya ruwaito shi], kuma abinda yafi falala ga alhaji shine kada ya azumce shi; domin koyi da aikin Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi, kuma domin wanzar da ƙarfinsa domin yayi ƙoƙarin yawaita ƙanƙan da kai da addu'a.

Kuma ranar Arafah mahaɗar musulmai ne wanda yake abin shaidawa, ranar fata daga Allah da jin tsoron Allah, da ƙasƙantar da kai da sassaukar da kai, rana mai karamci ga musulmai domin "babu wata rana wanda Allah yake yawaita 'yanta bawa daga wuta a cikin ta kamar ranar Arafah"[Muslim ya ruwaito shi], Shehun Musulunci Allah Ya jiƙansa ya ce: "alhazai a yammacin ranar Arafah abinda ke sauka a cikin zukatansu na imani da haske da albarka ba zai yiwu a iya bayaninsa ba".

Kuma addu'a tana da girman matsayi da ɗaukakan sha'ani; bawa yana miƙa buƙatunsa zuwa ga Majiɓincinsa kuma yana roƙonSa daga karamcinSa mai gudana koda yaushe, kuma yana

fuskanta zuwa ga Allah da zuciyarsa yana mai biyayya ga umurnin Allah na cewa:

﴿فَادْعُوا اللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ الدِّينَ﴾

"to ku kira Allah kuna masu tsarkake addini a gare Shi", to ka miƙa roƙonka zuwa gare Shi, kuma ka gana da Shi game da baƙincikinka, kuma a cikin ranar Arafah da waninsa, kuma ka sami yaƙini na tabbacin amsawa, kuma kayi naci ga Mai karamci wajen neman buƙata, domin Shine Mai yawan halitta Mai cikan sani:

﴿إِنَّمَا أَمْرُهُ إِذَا أَرَادَ شَيْئاً أَنْ يَقُولَ لَهُ كُن فَيَكُونُ﴾

"yanda al'amarinSa yake shine idan Ya nufi wani abu Ya ce masa kasance sai ya kasance". Ibn Abdilbarr Allah Ya jiƙansa ya ce: "addu'ar ranar Arafah karɓabbe ne dukkansa mafi rinjaye".

Kuma a cikin kwanaki goma na Zul-hijjah akwai ranar Salla babba; mafi girman ranaku a wurin Allah; Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "lallai mafi girman ranaku a wurin Allah shine ranar soke Sallah babba"[Abu Dawuda ya ruwaito shi], kuma shine mafi tsananin haramtuwar ranaku a wurin Allah, Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce a cikin huɗubar hajjin bankwana ranar soke dabba: "ku

saurara lallai mafi haramtuwar ranaku shi wannan ranar da kuke ciki, kuma mafi haramtuwar watanni shine wannan watan da kuke ciki"[Ahmad ya ruwaito shi], kuma shi ɗaya ne daga cikin idi biyu na musulmai, ranar farin ciki da murna domin aikata wani rukuni daga cikin rukunnan Musulunci.

Kuma shine mafi falalar ranakun ayukkan hajji, kuma mafi fitowarsu fili, kuma mafi taruwar jama'a a cikinsa, kuma shine ranar hajji mafi girma, Wanda Allah Ya ce game da shi:

﴿وَأَذَانٌ مِنَ اللَّهِ وَرَسُولِهِ إِلَى النَّاسِ يَوْمَ الحَجِّ الأَكْبَرِ﴾

"kuma sanarwa daga Allah da ManzonSa zuwaga mutane a ranar hajji mafi girma".

Kuma a ranar Sallah babba ne Allah Ya ba AnnabinSa Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi labarin cewa Ya kammala masu addini wato basa buƙatar wani ƙari har abada, kuma haƙiƙa Allah Ya cikashi kuma baZai rage shi ba har abada, kuma Ya yarda dashi ba Zai ƙishi ba har abada, sai wanda Tsarki ya tabbata a gare shi Yace:

﴿اليَوْمَ أَكْمَلْتُ لَكُمْ دِينَكُمْ وَأَتْمَمْتُ عَلَيْكُمْ نِعْمَتِي
وَرَضِيتُ لَكُمُ الإِسْلاَمَ دِيناً﴾

"a yau Na kammala maku addininku kuma Na cika maku ni'imaTa a gare ku kuma Na yardar maku musulunci a matsayin addini" Ibn Katheer Allah Ya jiƙansa ya ce: "wannan itace mafi girman ni'imar Allah Mabuwayi da ɗaukaka ga wannan al'ummar; ta yanda Maɗaukaki Ya kammala masu addininsu, sai ya zamo basu buƙatar wani addinin koma bayansa, kuma basu buƙatan wani annabi koma bayan Annabinsu".

Kuma kowane Annabi Allah Zai tambaye shi ranar Alƙiyama game da isar da sako ga al'ummarsa, Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "kuma ku za'a tambayeku game da ni"[Muslim ya ruwaito shi], kuma a ranar Salla babba Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya tambayi sahabbansa sai yace: "shin na isar? Sukace: Eh, yace: ya Allah Ka shaida"[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma a wannan ranar mai girma Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi yayi wisiyya ga al'ummarsa da cewa su isar da addininsa ga mutane, sai yace: "to sai wanda ya shaida ya isar ga wanda bashi nan; ta yiwu wanda za'a isar ma yafi kiyayewa sama da wanda ya shaida"[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Muzhiry Allah Ya jiƙansa ya ce: "kuma wannan kwaɗaitarwa ne akan

koyar da mutane hadisan Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi da wasunsa na daga ilimomin shari'ah, domin lallai ba don karantarwa ba da koyon karatu da ilimi ya yanke tsakanin mutane".

Kuma tare da farin cikin mutane da idi ta yiwu wasu daga cikinsu su rafkana daga ambaton Allah, Wanda tsarki ya tabbata a gare Shi Ya ce:

﴿وَاذْكُرُوا اللَّهَ فِي أَيَّامٍ مَعْدُودَاتٍ﴾

"kuma ku ambaci Allah a cikin kwanaki ƙididdigaggu", Ibn Abbas Allah Ya yarda dasu ya ce: "kwanaki ƙididdigaggu: sune kwanakin busar da nama, kuma su kwanaki uku ne bayan ranar soke dabbobi", kuma Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "kwanakin busar da nama: kwanaki ne na ci, da sha, da ambaton Allah"[Muslim ya ruwaito shi], Ibn Hajar Allah Ya jiƙansa ya ce: "kuma haƙiƙa falala ta tabbata ga kwanaki goma, sai bisa wannan falala ta tabbata ga kwanakin shanya nama".

Kuma a cikin kwanakin soke dabbobi da shanya nama akwai bauta ta dukiya ta jiki wacce itace mafi soyuwan aiki a wurin Allah, Allah Ya gwamata da sallah; sai Wanda tsarki ya tabbata a gare shi Yace:

﴿فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَانْحَرْ﴾

"to kayi sallah ga ubangijinka kuma ka soke dabba", kuma haƙiƙa Allah Ya kwaɗaitar akan tsarkake niyya a gare Shi lokacin soke dabba, da kuma cewa manufar ta kasance neman yardar Allah ne Shi kaɗai, ba taƙama ba, kuma ba riya ba, kuma ba jiyarwa ba, kuma ba zallar al'ada ba, sai Wanda tsarki ya tabbata a gare shi Ya ce:

﴿لَنْ يَنَالَ اللَّهَ لُحُومُهَا وَلَا دِمَاؤُهَا وَلَكِنْ يَنَالُهُ التَّقْوَى مِنْكُم﴾

"namominsu da jinanensu baza su sami Allah ba sai dai abinda ke samunSa shine tsoron Allah daga gareku", kuma "Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi yayi layya da raguna biyu masu yankan batta masu kahoni, ya yanka su da hannunsa"[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], ma'anar am'lahu: shine baƙi wanda saman gashinsa akwai fari, shi kuma al'aƙranu: shine mai ƙaho.

Kuma mafi falalar layya: mafi tsadansu a farashi da mafi darajarsu a wurin ma'abotansa, kuma Musulmi kada ya nuna jin damuwa game da tsadar farashin su, domin ladanta a wurin Allah yana da girma, kuma tunkiya ɗaya tana wadatar da mutum da mutanen gidansa, kuma ba laifi idan

mutum ya ci bashi domin yayi layya, to ku ji daɗi a ranku da ita, kuma ku ci, kuma ku ciyar, kuma kuyi sadaka, kuma ku kirdadi mabuƙatanku wajen sadakokinku, kuma da kyaututtukanku daga cikinsu ga makusantanku da maƙwabtanku.

Kuma wanda yayi nufin yin layya daga cikinku ya haramta a gare shi a cikin kwanaki goma ya cire wani abu na gashinsa ko ƙumbarsa, Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "duk wanda ya kasance yana da abin yanka da zai yanka, to idan jinjirin wata Zulhijja ya fito, to kada ya cire wani abu daga gashinsa ko kuma daga ƙumbarsa har sai yayi layyar"[Muslim ya ruwaito shi].

Kuma haɗarin zunubbai yana girmama da aikatasu a lokutan samun rahmah da alkhairai; Wanda tsarki ya tabbata a gare shi Ya ce:

﴿إِنَّ عِدَّةَ الشُّهُورِ عِنْدَ اللَّهِ اثْنَا عَشَرَ شَهْراً فِي كِتَابِ اللَّهِ يَوْمَ خَلَقَ السمَوَاتِ وَالأَرْضَ مِنْهَا أَرْبَعَةٌ حُرُمٌ ذَلِكَ الدِّينُ القَيِّمُ فَلَا تَظْلِمُوا فِيهِنَّ أَنْفُسَكُمْ﴾

"lallai yawan watanni a wurin Allah watanni goma sha biyu ne a cikin littafin Allah ranar da Ya halicci sammai da ƙasa daga cikinsu akwai haramtattu guda huɗu wannan shine addinin Allah

tsayayye to kada ku zalunci kawunanku a cikinsu", Ƙatada Allah Ya jikansa ya ce: "zalunci a cikin watanni haramtattu zunubi ne kuma laifi ne mafi girma akan wasu lokutan komabayansu, kuma duk da cewa zalunci a kowane yanayi yana da girma, sai dai Allah Yana girmama abinda Yaso daga cikin al'amurranSa".

**Bayan haka yak u Musulmi**:

Wanda yaji daɗi shine wanda ya ribaci lokutan keɓantattu a cikin watanni da kwanaki da sa'oi, kuma ya nemi kusanci zuwa ga Majiɓincinsa da abinda ke cikinsu na ayukkan ɗa;a.

**Ina neman tsarin Allah daga shaiɗan jefaffe**

﴿سَابِقُوا إِلَى مَغْفِرَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ وَجَنَّةٍ عَرْضُهَا كَعَرْضِ السَّمَاءِ وَالأَرْضِ أُعِدَّتْ لِلَّذِينَ آمَنُوا باللَّهِ وَرُسُلِهِ ذَلِكَ فَضْلُ اللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَاءُ وَاللَّهُ ذُو الفَضْلِ العَظِيمِ﴾

"Kuma kuyi rige-rige zuwa ga wata gafara daga Ubangijinku da wata aljannah faɗinta kamar faɗin sama da ƙasa an tanadeta ga waɗanda sukayi imani da Allah da ManzanninSa wannan falalar Allah ce Yana bada ita ga wanda Yaso kuma Allah Ma'abocin falala ne mai girma".

Allah Yayi albarka a gare ni da gare ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah bisa kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi bisa datarwarSa da baiwarSa, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Shi kaɗai baShi da abokin tarayya ina mai girmamawa ga al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawansa ne kuma Manzonsa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da sahabbansa kuma da Aminci mai ƙaruwa.

**Yaku Musulmi:**

Ita tuba tana da matsayi mai girma a cikin addini; domin itace sababin cin nasara da arziki, Allah Ya wajabta ta akan dukkan bayi daga dukkan zunubbai, sai Yace ga wanda yayi masa iƙirarin mata da ɗa:

﴿أَفَلَا يَتُوبُونَ إِلَى اللَّهِ وَيَسْتَغْفِرُونَهُ﴾

"shin bazasu tuba zuwa ga Allah ba kuma su nemi gafararSa?", kuma Yacema muminai:

﴿وَتُوبُوا إِلَى اللَّهِ جَمِيعاً أَيُّهَا الْمُؤْمِنُونَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ﴾

"kuma ku tuba zuwa ga Allah dukkanku ya ku muminai ta yiwu ko kun sami cin nasara", kuma Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana roƙon Allah sau ɗari cewa ya karɓi tubarsa; Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "ya ku mutane, ku tuba zuwa ga Allah, domin lallai ni ina tuba zuwa gare Shi a rana sau ɗari" Wato ina cewa: ya Ubangiji ka karɓi tuba na [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma lallai mu munfi buƙatar tuba, kuma mafi alkhairin kwanakin mutum shine ranar tubarSa; Annabi Yabo da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya cema Ka'ab bn Malik Allah Ya yarda da shi: "ka busharantu da mafi alkhairin ranar da ya shuɗe maka tun da mahaifiyarka ta haifeka"[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma mai ya kai kyawu ga mai tuba ya tuba a mafi soyuwar ranaku a wurin Allah! Kuma duk wanda yayi gaskiya a cikin tubansa; zai ɗaukaka a wurin darajoji, kuma Allah Zai canza zunubbansa zuwa kyawawan aiki.

Sannan ku sani cewa Allah Ya umurce ku da yin salati da neman tsira ga AnnabinSa....

# خطبة الجمعة

٥/١٢/١٤٤٤هـ

2023/4/21 م






فضيلة الشيخ

د. عبد المحسن بن محمد القاسم

إمام وخطيب المسجد النبوي الشريف


بعنوان

# أعمال عشر ذي الحجة

مترجمة بلغة هوسا